*FCWA ☀️*

#Sadaukarwa ga duk waɗanda suka taɓa rasa wani jigo nasu a soja.Allah jadadda rahama a gare ka Yayana AbduRashid😓

*Ƙirƙiraren labari ne,bai faru ba a gaske .Ban yarda a juya shi ko a mayar da shi audio doli sai da izinina*

1-2

A nutse nake sauraren mahaifiyata ido a lumshe,tun da ta fara nasihar nake daɗa jin nutsuwa na sake samun gurbi a zuciyata har sai da ta zo da furucinta na ƙarshe wanda yayi tsananin razana ni har ban san lokacin da na furta "mi kika ce Ammy?" na yi tambayar da tunanin ko kunnena ne bai jiye min daidai ba.

"A yau an ɗaura aurenka da Maryama ina so ka riƙe amana zuwa gobe in sha Allah zan kawo ta da kaina" ta sake maimaita wa,shiru na yi ina jin wani yanayi marar misaltawa.

"Ibraheemu haƙuri za ka yi, wannan ne kawai gatan da za mu yi wa Maryama don nuna soyayyarmu gare ta da kuma jadadda girman alƙawarin da na ɗaukar wa mahaifiyarta kafin ta bar duniya" yanzu ma dai shiru na yi ba don ban ji ba sai don abubuwa da dama da suka dinga gwaro a kwanyata.

"Heemu ka na ji na kuwa?"
"Na'am Ammy ina ji" na faɗa ina jan ajiyar zuciya,ita ma ajiyar zuciyar ta sauke kafin ta ce " ina Daddyn ka?"
"Ya fita tun jiya bai dawo ba"
"Okay sai an jima "
"Ammyyy!" na faɗa da sauri,sai ta tsaya da ƙoƙarin kashewar ta ce " ya aka yi yarona ina jin ka?"
Kamar mai koyon magana na ce "ki bar ta nan wurin ki har zuwa wani lokaci "
"Saboda me?"
"Kawai Ammy "
"Sai mun zo" ta faɗa tare da kashe kiran na furzar da huci ina jin duniyar na juya min.Screen ɗin wayar na ƙurawa ido ina kallon hotonmu wanda shine hoton ƙarshe da muka ɗauka tare da ɗan uwa kuma abokina.

«Zo mu ɗauki hoto ina jin a jikina kamar ba zan fito daga wannan yaƙin ba»cewar Abakar ya na dariya,wacce ba ta kai ga gushe wa ba na yi amfani da wayata na ɗauke mu selfie.Hoton na

shafa yayin da kuma muryarsa ke yi min amo a dodon kunne,da sauri na miƙe na nufi ɗakin motsa jiki na soma training.Na shafe kusan awa biyu kafin na fito na wuce bedroom wanka na yi na shirya cikin t-shirt ta soja da wandon kaki.Key ɗin mota na ɗauka kafin na sauko ƙasa inda ƴan aiki ke ta shawagi,su na gani na suka soma gaishe ni kamar kullum da kai kawai na amsa masu na fita zuwa harabar gidan.

Inda motata ke parker na nufa direct, ɗaya daga cikin escort ɗin ne ya rugo ya na tambaya ta inda zan je.“ Ni kaɗai zan tafi babu buƙatar rakiya ko ba ga cikin kayan da nake ba?”
“Sorry mai gida yalɓai ne ya bada umarnin duk inda za ka je mu yi ma rakiya” ya faɗa cike da girmamawa.
“Yi tafiyar ka” na faɗa tare da shige wa ciki na yi wa motar key,wurin fita ma sai da sojawan da ke tsaron ƙofa suka ɓata min lokaci kafin su bar ni na fita.

A hankali nake gudu ina duba yanayin garin da yadda al'amurra ke tafiya,a haka har na isa barikin soja.Daidai ɗakinmu na yi parking,na jima sosai kafin na fito ,key nasa na buɗe ƙofar na shiga a nan take duk wani tsohon tarihi ya dinga dawo min.Dakyar nake cira ƙafa ina takawa izuwa ciki,daidai akwatinsa na je na tsaya tare da buɗa shi na ciro kakinsa mai ɗauke da sunansa Abakar.Na rungume rigar ina jin ƙamshin jikinsa na ratsa hancina,karon farko da na ji idona sun cika da hawaye tun bayan dawowar mu daga yaƙin da ya zame mana shamaki ni da abokina.

Sosai nake hawaye ina jin dutsen da ya jima da yin gini a zuciyata na motsawa haɗi da zubar da tururi .

“Ibraheem!” ya kira sunana a dake,duk da na san ko wane ne bai sa na juyo ba har lokacin da nake jin takunsa na matso ni.
“ Mi yasa ka fito alhalin na ce ka zauna gida? Shi ne kuma ka hana escort su take ma baya,mi yasa ba ka jin magana ta? In fa wani abu ya same ka?”

Sai a lokacin na juyo muna facing juna,ban ce masa komai ba sai idona masu cike da baƙin ciki da zafin ɗaukar fansa na ƙura masa.
“ Wannan zuciyar da kake ji da ita kar ka manta ni ka gado amma shine don tsageranci za ka ƙure ni da ido ka na kallo kamar sa'an ka.Abakar ya mutu ba shine sojan farko da ya taɓa rasa rayuwa ba a wurin yaƙi amma duk ka bi ka adabi mutane da hauka,shi Abakar ɗin wa ya fi ne da ba za a kashe shi b...”
“Daddy???” na faɗa a zuciye kafin kuma na juya na mayar da rigar C
cikin akwati na rufe na sungumi akwatin na fito,don yanzu shi ne kawai abin da ya rage min nasa.

Bayan mota na saka shi,sam ban damu da tarin sojawan da suke tsaye ba waɗanda na san

tare suke da mahaifina.Ko ɗakin ban koma na rufe ba na yi wa motar key,ina tafe ina tunanin ƙiyayyar da Daddy ya ɗorawa Abakar dare ɗaya wacce a can farko ba haka suke ba.
Na ja wani huci ina mai danganta abin da don ya fito gari guda ne da mahaifiyata,a haka na isa gida can sama na haura da akwatin na ajiye shi bisa bed ɗina.

Gaban mirror na je na yi tsaye na ƙurawa fuskata ido wacce ta ƙara yin ja don ɓacin rai,baƙar sumar kaina mai tarin yawa na hargitsa ina kai wa ƙaton ƙirjina duka ina mai yin wata hargowa kamar kumurcin  zaki har manyan damatsana su na masu motsawa.

Wayata ce ta ɗau ruri sai da ta yi na uku kafin na ciro ta na ɗauka hadɗ da karawa a kunne.
"Ka sauko ƙasa ina son yin magana da kai" shi ne abin da ya faɗa kafin ya kashe, toilet na shiga na wanke fuska ta kafin na sauka ɗin.A zaune na tarar da shi ya ɗora ƙafa ɗaya kan ɗaya,shi ma sanye yake cikin na soja mai ɗauke da adon galolin yabo birjit.Kujera mai facing tasa na zauna ina mai sunne kai saboda sai yanzu ne na ji ban kyauta ba game da abin da na yi masa.
"Ibraheem ka ɗago ka kalle ni" yayi furta cike da kulawa,ƙin ɗagowar na yi saboda kallon tsakiyar idon Daddy sai mutum ya shirya,na sha jin sojawa na faɗar su na shakkar kallon nasa wanda ni ma shaida ne ba a ko wane irin yanayi ba ne nake iya kallonsa.

"Mine ne damuwar ka? Abakar?"
Sai a lokacin na ɗago na dube shi,murya cike da rauni na ce " Daddy shi ɗin abokina ne tun na ƙurciya ina mugun sonsa,tamkar yadda Wa ke son ƙanensa..." shiru na yi ina jan ajiyar zuciya.

Daddy ya ce " saboda mutuwarsa ce nake ganin rauni a idon ka? Ka gaji ne da aikin sojan na tsige ka?"
Wani irin halbawa zuciyata ta yi,da sauri na ce " haba Daddy ya za ka ce haka? In na bar aikin soja mi zan yi ?"

Ya miƙe tsaye ya na cewa "to in ka na son ci gaba da zama a ciki,ka fidda Abakar a ranka ko sunansa kar na sake jin ka ambata" har ya kai bakin ƙofa kuma sai ya juyo muna kallon juna kafin ya ci gaba da cewa "zuwa an jima sabuwar mahaifiyar ka za ta tare ban son jin wata matsala ta fito daga gare ka" ya na gama faɗa ya fice.

Tsakanin baƙin cikin sharaɗin da ya gindiya mini da kuma kishin Ammyna da nake yi jin zai kawo wata mace matsayin mata sai na rasa da wanne zan ji.Ɗaki na koma na kunna  karatun Alkur'ani ina saurare,a haka bacci ya ɗauke sai wuraren sallar zuhur na farka.Na yi wanka hadɗ da alwala na saka jallabiya na wuce masjid da ke nan cikin gidanmu,ni na ja su sallah bayan mu gama na zauna nan na ci gaba da lazumi ban fito ba sai bayan sallar Asar.

“Babana yau mi za a girka ma na buɗa baki?” Granny ta tambaye ni,mahaifiyar Daddy ce a nan gidanmu take zaune tun kafin ma a naɗa shi komanda sojoji.Muna gane wa juna ni da ita don ni ɗaya ne kaɗai jikanta,kaf ƴaƴanta kuma tun su na jarirai suke mutuwa Daddy kawai ya tsaya.

“Tsohuwa mai ran ƙarfe ina kika shige duk yau ban gan ki ba” na faɗa tare da nufar ta ina ta ƙoƙarin ƙaƙalo murmushi.
“Ina ɗakina,ai ba ka neme ni ba tun jiya ƙafar nan ta matsa min da ciwo” ta faɗa ta na nuna min ƙafar wacce ta ɗan kumbura.
Kan capet na zauna na soma matsa mata ƙafar,cikin sigar zolaya na ce “ko sai an yanke ƙafar nan dai?” ta dungure min kai ta na mai cewa “ka ji min shashanci in an cire gobe da mi zan tarben amaryar ka?”
Fuska na kwaɓe ina mai kallonta,ta sakar min murmushi ta ce “Ammyn ka ta kira ni ai ,t sanar da ni yadda kuka yi da ita.Ka na ji Babana ita wani sa'in rayuwa ita ke tsara mana yadda za mu yi,ba kowanne lokaci ba ne abin da mu muka tsara zai zamana daidai” sai kuma ta canza yanayin fuskarta kafin ta ci gaba da cewa “ka ɗauki misalin Daddynka mana,tun ya na yawo da ragga Maimuna ke sonsa kawai daga samun canjin rayuwa ya wulaƙanta ta ita kuma ta ɗauki abin da zafi mine ne na ɗaukar mataki maimakon ki bar wa Allah komai? ”

Na ja numfashi na ce “Granny wai mi ya gama Ammy da Daddy faɗa har suke gaba haka? ”
Ta shafi kaina ta ce,“Daddyn ka ya yi butulci,saboda amarya ya mari Ammyn ka  da ta so nuna masa kuskuren yin haka ya lakaɗa mata na jaki a ƙarshe kuma ya danƙara mata saki.A ranar da za ta fita ta bugi ƙirji ta ce masa yadda ta fita daga gidansa,haka duk matar da zai auro za ta fita.Wai ka na da ma labarin yau wata amaryar zai kawo?” Granny ta buge da tambayata.

Ni kuwa tun da na ji wulaƙanci da tozarcin da ya yi wa Ammyna na soma jin tsohon fushina na sake bijirowa.Na yunƙura zan tashi,Granny ta yi saurin mayar da ni ta na cewa “ina kuma za ka je? Faɗa min abin da za a yi ma na saka ƴan aiki yanzu nan”
“Duk abin da kika zaɓa Granny ya yi” na faɗa tare da miƙe wa na haura sama.Ina shiga ɗakina na fahimci tabbas wani ya shigo ciki,to amma mi aka shigo yi? Kafin na kai ga lalubo amsa idona ya sauka kan bed sam babu akwatin da na ajiye.
Waya na ɗauko na soma kiran Daddy amma bai ɗauka ba,na fito da sauri ina tambayar Granny “ba ki ga wanda ya shiga ɗakina ba?”
“Lafiya mi ya faru?”
“Akwatina aka ɗauke” na bata amsa kai tsaye.
“Baturen nan ne dai ya ɗauko shi a gabana ya fita da shi”
“Joy?” na tambaye ta ta ce “eh shi fa” na dafe kaina,Joy shi ne  soja na hannun damar Daddyna.Da wannan takaicin na zauna zaman jiran shi,a nan falo na sha ruwa tare da taimakon Granny har na je na bayar da salloli na dawo babu ko motsin Joy.Mu na nan zaune ni da Granny,aka kawo amaryar Daddy wata ƴar ficiciya da ita ko kunyar aurenta bai ji ba.
A gaban Granny aka kawo ta ,tun daga danginta har ita amaryar ƴan iya yi ne Granny ta yi musu Allah sa albarka kafin ta nuna musu sashen Daddy suka wuce da ita.

Na dubi Granny cike da jin haushi na ce “yanzu wannan ce ya auro?”
“Babu ruwan ka,dama ya ce na ja ma kunne akan haka.Duk gani yake saboda tsamin ranka matansa ke fita daga gidansa,sam ya ƙi yarda aikin Maimuna ne”
Na ce “Granny ya za ki ce aikin Ammy ne?”
“ A bar zancen to.Mi ka shirya wa goben?”
Ban bata amsa ba sai kwanciya da na yi na ɗora kaina kan cinyarta,ta ce “sai son jiki kamar mage,ga ka dai ƙaroto amma da taɓi'a yara in ka karye ƙafar tawa ai shikenan”
Na yi ɗan murmushi na ce “granny don Allah yi min addu'a na yi bacci ko zan huta da baƙin cikin nan da nake ji”haka kuwa aka yi ta soma yi min karatu,duk da ta na tsohuwa haka take fitar da harufa yadda ya kamata.Sosai nake jin daɗin karatun sai dai baccin ya ƙi samuwa,a ƙarshe ma ita ce ta soma yin gyangyaɗi a doli na miƙe na yi mata rakiya ɗakinta sannan na wuce nawa.A wannan daren ban rumtsa ba sam, system na ɗauka na soma yin binciken da y shafi aikina har aka kira sallar asubah bayan na dawo daga sallah na ɗora daga inda na tsaya.Wuraren ƙarfe tara na tashi na yi wanka na shirya cikin ƙanana kaya wando jean da rigarsa ,ko agogo ban saka ba na fita.
[29/07 à 09:31] MRS SADAUKI 👑: *IBRAHEEM*
```soldier man```

© Chamsiya Laouali Rabo
#MRS SADAUKI💫✍️

*FCWA ☀️*

#Sadaukarwa ga duk waɗanda suka taɓa rasa wani jigo nasu a soja.Allah jadadda rahama a gare ka Yayana AbduRashid😓

3-4

Tun daga nesa nake ƙare musu kallo,sai kace wani ƙaramin yaro sai ririta amayar yake ya na bata abinci a baki ko kunya bai ji har da wani ɗora ta kan cinyarsa ita kuma uwar iya yi da rashin kunya ta na gyara masa hullar kansa.
Na ɗauke kaina,har na ida sauko wa daga kan benen ban kalle su ba ina shirin zama kan kujera na ji Daddy na wata irin dariya mai cike da tsantsar farin ciki ya na cewa “Baby ba fa haka ake ɗora hullar ba,na faɗa miki kan zakin can gefe yake kallo”
“Uhum!Umhum! Ni dai haka ta fi min kyau Baby” ta faɗa cikin wata shagwɓar da tasa na yi saurin ɗaga kai na kalle su ,aka kuwa ci sa'a shi ma Daddyn ya ɗago ya na kallon saitin da nake.Da ido na tsure shi da su rai ɓace,da sauri na ga ya sauke ta daga kan cinyarsa ya ɗora ta kan kujera.Ta taɓe baki ta na kallona,ashe kallon tsoro na yi mata a jiya tsohuwar yarinya ce ƙaramin jiki ne kawai da ita ta ci uban bleachin ta yi fayau.
```

“Ibraheem ka fito?” Daddy ya tambaye ni,ban amsa ba na fasa zaman na wuce part ɗin Granny ina jin zuciyata na tururi.A zaune na tarar da ita ta na shafa maganin ciwon ƙafa,na zauna kusa da ita ina mai gaishe ta ciki-ciki.
Ta amsa da “lafiya lau ka ci abinci ne?” na girgiza kai ta ci gaba da cewa “da kaina fa na zaɓi abin da za a dafa ganin jiya ba ka ci wani abin kirki ba” ban ce komai ba sai ƙafarta da na soma matsawa.

“Babana ban son shirun nan,faɗa min mi aka yi?”

“Daddy ne” na faɗa cike da takaici.
“Mi yayi kuma?”
“Shi da matarsa ne...” na cije leɓen ƙasa kafin na ci gaba da cewa “kamar wani ƙaramin yaro shine zai zo tsakiyar falo da girmansa da darajarsa ya na ba ƙaramar yarinya abinci a baki har da ɗora ta a cinya? Granny in ni ɗansa ne na kawar da kai su kuma ma'aikatan gidan nan fa?”

“Don Allah fita batun su,bani makullin ɗakin ka zan sa a ƙara gyara shi kafin Ammyn ka su ƙaraso” Granny ta faɗa .
Na ce “wato ke ma kin basa goyon baya ya ci gaba da yin haka?”
Granny ta ce “to mi kake so na ce Babana? Duk tsiyarsa dai ai ba zai koma saurayi ba,ban makulli ka ji”
“Wai yanzu gaske kawo ta Ammy za ta yi? Allah ni ban shirya wani zama da mata ba” na faɗa ina mai kwanciya kan lalausan capet ɗin.

Granny ta ce “yau na ga abin da ya fi ƙarfina wai tsohuwar da ƙirgen dangi! Yanzu Babana kai ne ba ka shirya zama da mata ba? To halan so kake sai ka zama tuzuru sannan?”
Na turo baki tare da lalubo key ɗin na miƙa mata na ce “ni dai wallahi inda ma wurin ki ta zauna”
Ta na dariya ta miƙe tsaye ta ce “tun da ni aka aura ma ita ba.Tashi mu je ka ci abincin”
“A kawo min nan ba zan sake fita na ga kayan takaici ba”
“Ka ji wani zancen mutum da matarsa,kai ma ai ka kusa hutawa da zamana gwabranci can a yi wa kaji zabbi hira suke” ban sake cewa komai ba har ta fita,can sai ga ɗaya daga cikin ƴar aiki ta shigo da sallama ta kawo min abincin.
Da kaina na zuba na ci sama-sama kafin na sha ruwa na haye katifar Granny,wani bacci ma na soma ji amma ina tunawa da Abakar ya bar duniya sai na ji ya fita idona.Da sauri na fito don tambayar Daddy inda yasa aka kai min akwatina sai kuma na tarar da shi a tsaye ya na kallon tv da ke manne a jikin bango.

Zuciyata har wani tsalle take tsabar yadda allurar soja ta motsa,bresking New ne ake ƴan ta'adda sun kai hari a wani ƙaramin ƙauye da ke cikin Zamfara sun kwashe shanu da kuma wasu samarin garin.

Daddy na kalla na ce “sai yaushe ne ƙasarmu za ta bar fuskantar ƙalubalen nan? Gagarar mutane ne suka yi ko rashin iya aikin jami'an tsaro ne?” kallona yayi ba tare da ya ce komai ba ya fita,da sauri na nufi matakalar da za ta sada ni da sashena.Bibiyu nake taka ta har na isa,ina shiga ɗakin na tarar da Granny da ƴan aiki su na ta gyaran falon direct bedroom na wuce nan ɗin ma akwai masu gyara shi.Falo na ce su koma na canza kayan jikina zuwa kakin soja,na saka takalmi da belt na ɗora hulla sannan na ɗauki baƙin gilashi na manna.Ƴar madaidaiciyar bindiga ta na ɗauko na soke a ƙugu kafin na fito,Granny ta tare ni ta na cewa “ina kuma za ka je?”
“Wani ɗan aiki za mu yi ki sa min albarka ”
“Allah tsare ya dawo da kai lafiya”
Na amsa da “amen kafin na fito”

Ina saukowa ƙasa na ji matar Daddy na waya “iyeee ke tsohon ɗan duniya ne inda kin ga yadda ya susuce jiya a kaina,na san tun da yake aure-aurensa bai taɓa samu mace haɗaɗɗiya kamar ni ba”
Godiya na yi ga Allah da falon babu kowa masu tsaron gidan duk su na waje,da wannan takaicin na fito na ɗauki motata na bata huta.
Sai da na hau kan titi sosai sannan na daidaita gudun motar na kira Ammy,har ta tsinke ba ta ɗauka ba sai a kira na biyu.
“Ina kwana Ammy kin tashi lafiya?” na faɗa cike da kwantar da murya.
“Lafiya lau alhamdullah! Ga mu a mota muna hanya ina ta bacci sai da Maryam ta tashe ni” cewar Ammy,na ɗan jan numfashi na ce “Ammy ni da na so na ce ku ɗan jira kar ku zo yau”
“Saboda me?”
“Ammy jiya fa Daddy ya kawo wata” na faɗa ina cije leɓena na ƙasa.
Ta ce “ina ruwana da matarsa? Ai ni bai gabana ballantana wata can banza”

“Zan sake kiran ki in na sauka Allah tsare hanya” na faɗa ,bayan ta yi min addu'o'in da ta saba na kashe.Ina isa can babban Barack na tarar da sojawa birjit duk sun yi uban layi,na san bai wuce umarnin Daddy ne ya na son tura su can inda abin ya faru.
Mota na parker sannan na nufi hanyar da za ta sada ni da ofishinsa,duk da ya na mahaifina sannan kuma na kasance soja hakan bai hana masu tsaron ƙofar hana ni shiga ba.
“Shi ne ya bada umarnin kar wanda ya shiga”
“ Ku bar ni na ce akwai maganar da za mu yi” na faɗa a karo na biyu,amma suka ƙi nan fa muka hau rigimar da ina tunanin ita ta jawo hankalin mutanen ciki har aka buɗe ƙofar.

Sergent Yakubu ne ya na ɗaya daga cikin waɗanda Daddy ke hulɗa da su ba a harakar aiki ba kaɗai,“ku bar shi ya shigo” ya faɗa ya na bani hanya don na wuce.Na yi musu kallon banza sannan na shige,a zaune na tarar da Daddy ya zube wasu duwatsu akan teburi alamu dabarun yaƙi yake shirya wa.

“Daddy?” na furta ,shiru bai amsa ba na sake cewa “Daddy ina son zuwa don Allah ka sa a tafi

da ni ” nan ma ɗin shiru yayi har sai da Sergent Yakubu ya ce “ shugaba za ka ce”
“Ka dai barsa ya ɗauka nan a gida muke”

Shiru na yi ina kallonsa,ya ɗago ya shi ma ya na kallon nawa kafin ya ce “ a gabana za ka tsaya da baƙin gilashi?”
“Ka yi haƙuri yalaɓai ban iya kallon tsakiyar idonka ne shi yasa,amma ina neman alfarma don Allah ka tsara tafiyar nan da ni”

“Captain IBRAHEEM Isa ba za ka je ba” ya faɗa tare da miƙe wa tsaye ya mayar da hankalinsa ga Sergent Yakubu ya ce “ daidai nan da nan za mu baza dakarun mu ta yadda za mu zagaye abokan hamayya,ka ga duk yadda aka yi dai mune da nasara in sha Allah saboda kowanne bango mun zagaye su”

“In kuma aka yi rashin sa'a kafin su isa su ƴan ta'addan sun bar wurin?” Sergent Yakubu ya tambaya.
Daddy ya ce “ har yanzu dai su na wajen kuma ba zata ce za mu yi musu ”

“An bi didigi an gano inda suke?” na yi tambayar ni ma ina ƙara matsawa,Daddy ya ɗago a hassale ya ce “ wai mi kake jira ne? Ba na sallame ka ba?”
“Don Allah Daddy ka bar ni na je”
“Ba za ka je ba fitar min daga ofis ko na sa a zo a fitar da kai ta tsiya ” ya faɗa cikin tsawa ya na nuna min ƙofa.
Amma abun ka da soja na dake na ce “ Yalaɓai mine ne amfanina kenan in har wata matsala za ta taso ba tare da na bai wa ƙasata kariya ba?”

“ Sai ka ajiye aikin tun da ba ka ga amfaninsa ba,Sergent Yakubu biyo bayana” Daddy ya faɗa tare da kwashe duwatsun kan teburin ya nufi wani ɗaki da ke cikin ofishin.Haka na bi su da kallo har suka shige ina jin lokacin da aka murɗa key ta ciki,na ja ajiyar zuciya tare da zagayawa na zauna kan kujerar da Daddy ke zama .Kamar an mitsike ni na jawo ɗan ƙaramin aljihun table ɗin,wani ƙonanen agogo na gani na ɗauke shi ina dubawa a kallon farko na gane na Abakar ne don ga farkon sunansa nan da na mahaifinsa a jikin ƙarfen kamar yadda duk wani soja da za a bai wa ita ake masa haka.Mayar da ita na yi na soma bincike har na kai ga liste ɗin sunayen waɗanɗa suka mutu,a nan ne na gano ita gawar Abakar sam ba a ganta ba.Jikina har rawa yake wurin maida komai yadda yake kafin na fito,tuni sojawan har sun shiga motoci riƙe da bindigogi.

Na je kusa da babban Sojan da ke kula da duk wani yaƙi ko tafiya in ta kama na ce “ a wacce mota zan shiga?”
“ Banda sunan ka a jerin sunayen da Shugaba ya bani ikon na tura” ya bani amsa.
“Saboda me?”
“Kila don ba ka daɗe da dawowa daga mission ba”

“Amma ya na ga har da waɗanda a tare muka dawo ɗin wasun su na ciki?”
Ya dube ni da kyau ya ce “ mahaifin ka za ka tambaya ba ni ba” ya na gama faɗa yayi gaba ya bar ni nan.Ina ji ina gani motocin suka fita suka bar ni,ina cikin wannan takaicin Daddy ya  aiko kira na.Ina shiga Sergent Yakubu ya fita ya bar mu,“zan saka wani aiki ne ka cike min takardun nan,sannan ka binciko min bayanai dangane da ƙauyukan nan” ya faɗa tare da miƙo min tulin takardu.Na karɓa har zan fita ya ce “zo ka zauna a nan ka yi” ban musa ba na ja kujera na soma cike takardun ,in jin idonsa a kaina amma na ƙi ɗagowa har sai da na ji muryarsa ya na cewa “Ammyn ka ta kira ni ...” sai kuma yayi shiru ya na kallona,na ce “mi ta ce ma?”
“Za ta zo nan gida”
Na ci gaba da abin da nake kafin na amsa masa da “eh na sani”
“Zuwan nata ne ba na tunanin zai haifar ɗa mai ido,ka san halin ta ba ta ƙaunar zaman lafiya”

“Shugaba wannan fa tsakanin ku ne bai kamata ka shigo da ni ciki ba” na faɗa ina mai kwashe takardun,na fita.
Motata na shiga ban zarce ko ina ba sai ɗayar Compagnie ɗinmu inda a can wurin kwana yake.Ɗakin na buɗe,duk yadda na so kar na yi tunanin Abakar abu ya cuttura.Rabi da rabi na yi aikin,sallah kawai ke tsayar da ni sai dab da magrib na fito na nufi gida.Bayan na yi parking sai da na ɗan zauna na wani lokaci kafin na fito,da sallama na shiga falon idona ya sauka kan Ammy.Da sauri na je gabanta na gaishe ina mai gaishe ta,cike da fara'a ta amsa ta na tambaya ta ya aikin na amsa “Alhamdullah”

Granny ta ce “baƙauyar amaryar ka ta zo,sai kuka take da rantse-rantse ita ba za ta haura saman bene ba”
Shiru na yi ban ce komai ba,na miƙe na ce “Ammy zan je na yi wanka lokacin magrib ya gabato”
“A fito lafiya” ta faɗa ,ni kuma na wuce na fara taka matakala kenan na ji muryar matar Daddy na cewa “Baby ga IBRAHEEM ɗin nan sai yanzu ya shigo,kaiii?” ta wani kira ni kamar ƙaramin yaro ko waigawa ban yi ba na idasa hayewa.
Ina tura ƙofar falon wani ƙamshi ya ziyarce ni,na lumshe ido ina shaƙar ƙamshin kafin na wuce bedroom.Allah na gani sam ban lura da ita ba sai da na ji uban ihunta,“na shiga uku na lalace mugun abu soja na a gabana?” ido kawai na zuba mata duk uban ihun nan na zata tsoro ta ji wai ashe murna ce take ta ga soja .Rikitatun idona na zuba cikin nata,da sauri na ga ta je bayan labule ta ɓuya kafin ta fara leƙe ban ce mata komai ba na je gaban mirror na yi tsaye idona na ga sun yi ja sosai.
“Je ki waje” na faɗa dakyar don so nake na canza kayan jikina .

Da gudu ta fita ta na bangaje ƙofa, cire uniform ɗin na yi kafin na shiga toilet wanka na yi haɗi da alwala sannan na ɗauro towel daidai ƙuguna.Kan bed na tarar da ita ta zuba uban tagumi,muna haɗa ido ta ja  blanket ta rufa ta na karkawa har gadon sai da ya dinga rawa ta ce “yi haƙuri....”cikin raunataciyar murya ta na mai fashewa da matsanancin kuka mai cin rai.
Na rumtse ido,a duniya in akwai abin da na fi tsana to kuka ne shi yasa ma ban cika son yara ba .Ina shirin fara shafa mai na ji sai ƙara ƙaimi take wurin kukan,zuciya cunkushe na nufi bed na zauna tare da yaye blanket ɗin.Da sauri ta yi baya ta na curewa wuri guda,kamar mai koyon magana na ce “ mine ne?” shiru ta yi bata bani amsa ba,“ ban son kukan nan ki yi shiru”

Cike da ƙurciya ta ce “ tsoro nake ji”
“Tsoron me?”
“Matakalar bene kuma ...kuma ni ban son nan wurin Ammy nake so kar ta tafi ta bar ni ban san kowa ba” ta bani amsa ta na shasheka kamar ranta zai fita.

“Ni wane ne?” na jefo mata tambayar ba tare da ni kaina na shirya ba.Ta buɗe fuskarta ta tsure ni da manyan idonta,kafin ta ce “abokin Ya Abakar wanda azzalumai suka kasheee” shaaa kuma sai wasu hawayen tare da ɗaukar wani sanfarin kukan.Ji na yi tamkar ta taƙalo min wata masifa daga can ƙasan zuciyata,raɗaɗin rashin Abakar ɗin ya dawo min sabo dal kamar yanzu ne aka shaida min mutuwarsa.A duniya tun da nake ni ban taɓa rarrashi ba,don banda ƙanwa sannan cikin aikin soja na girma ta yadda zuciyata ba ta san soyayya ba in ka fidda ta iyayena da kuma abokina.Rasa yadda za a yi na rarrashe ta na,kamar wani mai jin tsoro haka na jawo ta jikina tare da ƙoƙarin haɗe dafin da nake ji a cikin maƙogorona don na samu na yi mata magana.....
[29/07 à 09:31] MRS SADAUKI 👑: *IBRAHEEM*
```soldier man```

© Chamsiya Laouali Rabo
#MRS SADAUKI💫✍️

*FCWA ☀️*

#Sadaukarwa ga duk waɗanda suka taɓa rasa wani jigo nasu a soja.Allah jadadda rahama a gare ka Yayana AbduRashid😓

*YA Ubangiji rahama don ƙarfin ikonka ka wanzar da Zaman lafiya a ƙasata Nijar da Nigeria da ma duk sauran ƙasashen da ke fuskantar ƙalubalen rayuwar nan alfamar Manzon Rahama*👏🏻

5-6

“Yi shiru mana,ban son kukan nan Mary . Addu'armu ya fi buƙata a wannan lokacin,ki godewa Allah ɗan uwanki yayi mutuwar mazaje wacce ba kowa ne ke samun irin ta ba.Mutuwa a filin daga,domin kare ƙasarsa” na faɗa tare da ƙara janta jikina ina goge mata hawayen da suke ta faman yi mata zarya.
Cikin muryar kuka ta ce “ abokin Yaya ina cikin damuwa na rashin ɗan uwana,amma Ammy ta ce da kai da shi duk ɗaya ne duk kulawar da yake min kai ma za ka iya kuma zan fi jin daɗin zama da kai fiye da in zauna wurin ta”ta yi maganar ta na faman cusa kanta a ƙirjina.
```

Na ce “ eh gaskiya Ammy ta faɗa ,kin manta Abakar ƙanena ? Kin ga ke ma ƙanwata ce.Daga yau ban son ƙara ganinki ki na kuka,duk abin da kike so kuma ki sanar da ni”

Ta gyaɗa kai tare da cewa “ Ammy ta ce za ka kai ni ƙaton kanti ka saya min kaya”
Na ce “ eh sai in kin huta za mu je”
“ Yaushe kenan?”
“ Ko zuwa jibi haka”
“ Ba gobe ba?”
“ Za mu je goben to” na faɗa ina mai janye ta daga jikina tare da ƙoƙarin sauka daga bed ɗin,ta ce “ kenan kai ne mijina?”
Dariya tambayar ta bani,na ce “ Mary shekarun ki nawa?”
“Sha tara” ta bani amsa,na juyo ina kallon ta ban san mi yasa ba sai nake ji a raina ina son jan ta wasa na ce “ mai ƙarya dai ɗan wuta ne”
Ta buɗe baki ta na murmushi,na kafe ta da ido ganin fara'ar nan yasa na ji daɗi .
“ Na waɗa ma gaskiya ?”ta yi tambayar cikin Hausar ƙauyensu na Sokoto.
Na yi murmushi na ce “ eh faɗa min”
“Kai dai shekaruna Sha shida na”
“Sha shida ne za ki ce”
Ta turo baki ta ce “ ni wa ba zan iya yin Hausar ku ba,yawwa na ce ku nan kowa na da abun hawa na? Gari duk ko ina motoci na birjit awar an taso daga sallar idi ”

Ban bata amsa ba na soma shafa mai da turare,ta madubi nake hango yadda take kallona.Na yi gyaran murya na ce “ ki je ki ci abinci”
“ Ban jin yunwa”
“To koma falo zan shirya” da “toh” ta amsa ta fice.
Drower na buɗe na fiddo kayan da zan saka,ina tsaka da saka kayan kamar an ce in juya na hange ta ta na leƙe na.Muna haɗa ido ta tuntsire da dariya kafin ta gusa,na girgiza a zuci ina cewa ‘ yau na ga ikon Allah ’ bayan na gama na fita falon na tarar da ita a zaune ta ƙura wa ƙofar fitowa ido.

Na ɗan haɗe rai na ce “ mi yasa kike leƙe na?”
Ta sunne kai ƙila ta tsora ta da yanayin nawa,ta ce “ Ammy ta ce kar na ji kunyar ka kai mijina ne duk abin da za ka yi ni zan taya ka har saka kaya da wanka”
Na waro ido ina mamakin ya kuma Ammy za ta faɗi haka,na ce “ shi ne sai ki leƙe ni ?” ta ɗago kai ta ce “ to mine ne in na yi hakan kai ai mijina ne” sai ta soma wasa da awarwaron hannunta na duwatsu.

“ Na ji tashi mu sauka ƙasa” ta maƙe kafaɗa ta ce “ Allah tsoro naka ji”
“Nake ji ake cewa” na gyara mata da sauri kafin na miƙar da ita tsaye ta na turjewa muka fito.

“Kwarankwatse ba zan sauka ba” ta faɗa ta na shirin zubewa ƙasa ta riƙe ni gam.
Na ce “ to waye ya hauda ke saman?”
“Ammy ce da wata tsohuwa”
“To na ji ki nutsu babu wuya fa ki kalli yadda zan yi”
Ta ce “ Na wa san bene, kai hawar shi ta a ban yi saboda ina ganin jiri ”
Cak na ɗauke ta na soma sauka da ita ƙasa,ido ta rumtse gam har muka sauka na aje ta ina mai cewa “ baƙauya” Ammy da Granny suka saka dariya ni kuma na fita zuwa masjid.Ina can aka kira sallah,bayan an gama na shigo ciki muka je muka ci abinci gaba ɗaya Granny ta miƙe ta nufi ɗakinta.
Kusa da Ammy na dawo na zauna ji nake kamar kar lokacin ya shuɗe,“ Ammy yanzu tafiya za ki yi?”
“Tambayata ce kake?” ta faɗa tare da kallona,na gyaɗa kai. Ta ce “ zuwa gobe in sha Allah zan koma”

“Don Allah ki tsaya ko sati ɗaya ne ki yi” na faɗa .
Ta ce “ a'a ba zan jure ba Heemu,ɗazu ai ka ga rainin hankali da matar Ubanka ta yi yadda take wani kiran ka da gadara so ta yi na tanka mata don kawai a yi faɗa ”
Na ja numfashi na ce “ Ammy mi yasa ba za ki dawo nan da zama ba? Ban son ganin ku a rabe ke da Daddy ”

Sai da ta kalli Maryam kafin ta ce “ jeki sama Maryam ”
Ta ce “Ammy na dai je ɗakin waccan”
“Okay tashi ki tafi” ta miƙe da saurinta ta na gyara hijabinta wanda tun da ta yi sallah ba ta cire ba.

Bayan tafiyar ta ne Ammy ta dube ni da kyau ta ce “ faɗa mini matsalar ka”
“Babu Ammy ni burina kawai ki dawo nan ɗin” ta girgiza kai ta ce “ na bar Daddynka har abada,tun ka na goye na bar gidansa bai taɓa tunanin dawo da ni ba sai ni ce zan sarkawa? Ya je yayi ta aure-aurensa wata rana sai ya auro aljana”

“Ammy na sani Daddy yayi laifi amma hukuncin da kika ɗauka ne yayi tsauri sosai ” na faɗa cikin jimami ina tuno abin da Granny ta ce min game da mafarin rabuwar.

Ammy ta yi wani murmushin wanda ka ganinsa ka san na takaici ne kafin ta ce “ tun bayan da na koma gida bai taɓa tako ƙafarsa ba sai da ka shekara goma a ranar da ya zo ya tafi da kai ya saka ka makarantar sojoji,ya nuna min iko ya maido ka gidansa da ace ya na ra'ayina ai a tare zai maido mu” idonta ne na ga sun cika da hawaye,da sauri na miƙe ina cewa “ kuka kuma Ammy? Don Allah a'a” sai na shiga goge mata su.

Jiniya ce ta cika gidan alamun Daddy ya dawo,muna nan tare da Ammy amaryasa ta fito cikin murna.Daddy na shigo wa ta yi tsalle ta rungume shi ba tare da ko kunyar escort ɗinsa ba da suka yo masa rakiya.
Raina ne na ji ya sosu musamman da na ji Daddy na cewa “ za ku iya tafiya yanzu lokacin

iyalina ne" Ammy ta je ta miƙe na mayar da ita.

"Muuuah! Muuuah!" kawai kake ji amaryasa na masa kiss wanda ina da tabbacin da gayya take yinsa ,shi kuwa Daddyn kamar wani soko yayi tsaye na yi imanin bai lura da mu ba da tabbas ba zai tsaya ba.

"Mi kika girka min Bab..." sauran maganar ce ta laƙe a maƙoshinsa da muka haɗa ido da shi.Da sauri ya janye ta daga jikinsa " jeki ɗaki ina zuwa" ya faɗa ita kuma ta harare ni kafin ta wuce. Daddy ya wani haɗe rai ya na mai ƙaraso wa inda muke,na taɓe baki tare da barin wurin na fita zuwa masjid.

Daddy yayi gyaran murya ya ce "fatan kin sauka lafiya?"
Ammy ta ce " lafiya lau alhamdullah har ina shirin komawa ma"
Ya shafi gefen wuyansa ya ce " to madallah " Ammy ta ƙure shi da ido ta na kallonsa kafin ta ce "Isah sai yaushe za ka sanin ciwon kan ka? Aure-auren naka har ya kai ka auro karuwa wacce ba ta san mutumcin kanta ba? A gaban ɗan cikin ka kake sumbatar mace? Ayir ɗinka wallahi ka bani mamaki ...." Daddy yayi saurin katse ta da " don Allah Maimuna ban son tsiyar gumi.Ina ruwan ki da matata ? Wato kishi kike don kin gan kin koma tsohuwar akwala babu mashunshuni haushi ya kama ki kin ga na auri ƴar shilla?"
Sam ba su ga zuwan Granny ba sai saukar marin da ta kifa wa Daddy,ya dafe kumci ya na kallonta " Mama..." da sauri ta katse shi " rufe mini baki! Wato kai ba ka ƙaunar zaman lafiya daga ta na faɗa maka gaskiya shikenan sai cibi ya zama ƙari?"
"Wace gaskiya Mama ? Kawai banda ikon sakewa da matata?"
"A gaban ɗanka? In shiriritar kuke so mi zai hana ku yi ta can sashen ku? Kai yanzu ba zubewar girman ka ba ce da matsayinka da ikonka a gan ka kana abin yara? Dubi gemunka farin gashi ne ya fara tsiro wa amma a haka kake rungumar ƙanƙanuwar yarinya a gaban ɗan cikin ka.Maimuna mu je,ke ma da naki laifin ban ma san mi ya tsayar da ke nan ba" Granny ta faɗa tare da jan hannun Ammy suka koma can ɗakinta.
Maryam na zaune ta na karatun Alkur'ani,yanayin da ta ga Ammy ne yasa ta yi saurin rufewa ta nutsu sosai.

" Tashi ki koma sashen ku Maryam ki tabbatar kin yi wanka kin yi sallar isha'i kafin ki kwanta" cewar Ammy, Granny ta ce "a'a ki barta a nan har a jima"

Ammy ta ce " to ni zan ɗan kwanta " dama fashin sallah take hakan yasa Granny ba ta ce komai ba.Karatun suka ci gaba da yi ita da Maryam inda ta yi kuskure sai ta gyara mata,Maryam ta ce " ya aka yi kika iya karatu Kaka?"
"To in ba abin ki ba ta ya ba zan iya ba tun da ba makarantar Boko na yi ba mai zurfi"
" Tun ki na yarinya kenan kika iya?"

Ammy ta ce " Maryam ba a tsare babba da tambayoyi"

Granny ta ce “ a'a bar ta mana ita ma in ta tsufa haka jikokinta za su tsare ta da tambayoyi”

Maryam ta ce “ ni dai gaskiya ban so na tsufa” Granny ta dinga dariya ta ce “ ai baƙin gashin nan a sannu zai koma fari sol” Maryam ta hau kukan sangarta.
Ammy dai na jin su ba sake kula su ba,furicin Daddy sosai yayi mata tsaye a zuciya wai ta ƙi yin aure saboda babu mai sonta.Wasu hawayen takaici suka zubo mata a zuci ta ce ‘ in sha Allahu zan baka mamaki zan cire ka a rai na je na auri wani’ da wannan tunanin dai ta yi bacci.

A can ɓangaren Daddy kuwa cike da jin haushi ya nufi ɗakin amarya Zainabu,a yadda ya tarar ta ci uban shiri cikin kananan kaya sai ya nemi fushin ya rasa.Ita ma cike da iya yi ta zo ta rungume shi suka gama shiriritarsu,kafin ta yi masa rakiya zuwa toilet yayi wanka .Sai da ta cika masa tumbinsa sannan ya je masjid ,ganin IBRAHEEM ne yau zai ja su sallar ya ji haushi sosai don ya matsu ya koma ciki wurin amarya .

Cike da nutsuwa nake gabatar da sallar har muka kammala,kamar sauran lokuta a tare muke komawa gida ni da Daddy.Da sauri na miƙe na isa gare shi,ina son yi masa magana ne akan Ammy sai dai shi ya tari numfashina ya na mai cewa “ don Allah ka bar jan dogon karatu,wasu ba sa iya jurar tsayuwar nan ka yi ta karatu sai ka ce muna ƙiyamul laili?”yayi maganar ya na ɗaga ƙafa da alamu sauri yake.
Na ce “ yaushe soja ya fara tsoron tsayuwa? Duk sojawa ne sun saba dama to ai ni ban ga wata damuwa ba don an ja dogon karatu.Aka yi tsayuwa akan lamarin duniya sai wurin bautar Ubangiji ne za mu samu rauni?”

“To in fa mutum na da uzuri ? Irin hakan dai babu daɗi na faɗa ma”

“ Daddy na ga alamun kamar ka na sauri ga shi kuma ina son yin magana da kai” na faɗa ina jan numfashi daidai nan muka iso ƙofar da za ta sada mu da babban falon gidan.
“Ya ce ba yanzu ba ka bari zuwa gobe”
“Amma Daddy...” shiru na yi sakamakon ganin amaryar ta sake fitowa cikin wata shiga ta riga da wando duk sun matse ta rabin mamarta duk a fili .Da sauri na kawar da kai ganin ta rungume mahaifina duk da kuwa ƙoƙarin hanata da ya so yi,“ Haba Zee ya za ki fito haka wuce gani nan zuwa”
“ Ni dai... Ni dai Baby na ƙi wayon mu je ƙafarka ƙafata na sh....” sauran maganar ban ji abin da ta ce ba,na fi zaton Daddy ya toshe mata baki ne.
“ To na ji na baka minti biyu” ta faɗa kafin kuma na ji ƙarar takalminta alamun ta tafi.

“ Ibraheemu mi ka ce?” Daddy ya tambaye ni a ɗan daburce,sai yanzu na juyo na kalle shi da jajayen idona da suka rine tsabar ɓacin rai .A nan tsaye na barsa na wuce part ɗina, matakalar ma ban ganin ta da kyau.
Ina shiga ɗakina direct bedroom na wuce na kwanta rairan ina kallon sama,zuciyata sai tuƙuƙi take.
‘ Wai mutumen da in za ka gansa sai ka yi fiye da sati guda ka na shan wuya,mutumen da in

shugaban ƙasa zai fita sai ya bayar da izinin zai iya fita babu wata matsala,mutumen kowanne soja jininsa a akaifa yake in ya aiko kiran ka ko kuma in ransa ya ɓace shine waccar abar take cewa ta basa minti biyu?' na yi wa kaina tambayar a zuci ina jin farashin ƙunci,baƙin ciki da takaicina su na ƙara yin sama.

A daidai wannan gaɓar mutum ɗaya ne kacal ke saurin yin nasara kaina wurin sauke fushina,yanzu kuma ba ya tare da ni mutuwa ta yi mana yankan ƙauna.Haka na ci gaba da juyi a bed ina ta ƙoƙarin tunkuɗe lamarin amma abu ya cuttura,sama da awa biyar ina cikin hali guda.Dakyar na miƙe na je na shiga toilet,ko kayan jikina ban cire ba na sakarwa kaina shower.Ina nan daga tsaye na ji kukan Maryam,Ammy kuma na yi mata faɗan doli ta koyi hawa bene sannan ta jaddada mata nan ne ɗakinta kar ta saki ta kwana ɗakin Granny.

Ina jin lokacin da ita Maryam ɗin ke cewa " Ammy shikenan ba zan sake komawa bacci ba tun da kin tashe ni"
Ammy ta ce " ni ma ai don baccin ya sace ni ne amma ai sam da ba zan bari ki kwanta can ba,ki tabbatar kin yi wanka kin yi brush kafin ki kwanta" tsit kuma ban sake jin sautin muryoyinsu ba.

Na ja ajiyar zuciya kafin na tuɓe na yi wankan soso da sabulu na fito ɗaure da towel a ƙugu ,ɗan ƙarami kuma ina tsane gashina.
Zaune na tarar da ita ta buɗe trolly duk ta zubar da kayan da ke ciki sai wani turo baki gaba take,gaban dressing mirror na tsaya na yi shafe-shafe sannan na zaɓo kayan bacci masu riga mai sauka har ƙasa.Ina ganin lokacin da ta shiga toilet matse da kayan da za ta canza,da wannan ni ma na saka nawa kafin ta fito na je na haye bed bayan na kashe ƙwan lantarki sai na kunna fitilar bacci.
Tunani na soma yi kan shuɗaɗɗiyar rayuwarmu ni da Abakar,«aboki don ba ka da ƙanwa ne da ka ji irin yadda nake ji,Maryam komai ce nawa.Farin cikinta ya fi min komai daɗi a duniya,aikin nan ma domin ita da Umma nake yinsa.Na ci burin yi wa Maryam kayan ɗaki na kece raini a matsayina na waliyinta maɗaurin aurenta» wannan na ɗaya daga cikin zantukan da yayi min game da Maryam.
Yadda ta fado jikina ta bi ta kaina yasa ta katse min tunanin," ni wallahi sanyi naka ji ba don na yi wa Ammy alƙawarin ba,in na yi wankan nan shegiya nakai " ta faɗa cikin mita tare da gyara kwanciyarta ta ja bargon da nake ciki ta rufa.Duk da ta rufa ɗin bai hana ta rawa sanyi ba,kamar wanda aka yi wa doli na ɗan matsa kaɗan sai gani kusa da ita sosai.A hankali na ɗan kwanta ta samanta na yi mata rumfa da ƙirjina,hannunta na ji gefen cikina ta sarkayo shi haɗi da riƙe wa gam ta ce " ina jin sanyi sosai"

Bargon na ida ja ya rufe mu har wajen kai,a hankali kuma na matsa fuskata kusan tata ta yadda muna jin numfashin juna.Ƙamshin turarenta ne ya sakar min wata kasala da na kusanci wuyanta,ban san lokacin da na saki wani gauron numfashi ba ina mai sake saka ta ƙirjina.Tuni Maryam ta fara mitsirniya,gefen wuyanta na soma aika ma sumba kafin na yi sa'ar lalubo bakinta na fara kissing.Sam ba ta yi ƙoƙarin hana ni ba da alamu ma ta na jin daɗin haka don

sai ƙara riƙe ni take, wannan yanayin da na tsinci kaina sam ba zan iya faɗar yadda yake ba.Bugun zuciyata ne kawai ke ta tsananta ya na bada sauti na musamman,sama da minti talatin kafin na janye daga jikinta na koma gefe ina mayar da numfashi.Blanket ɗin na janye na maido shi iya ƙirji,idona a lumshe ina jin raina yayi ɗan sanyi ba kamar ɗazu ba.Na kai hannu na jawo ta na ɗora kanta kan ƙirjina yayin da kuma hannuna ke kan bayanta.Murya can ƙasan maƙoshi na ce " kin bar jin sanyin ?" kamar wata munafuka ta ce min " eh!" " ok yi bacci" " uhumm !" shiru duk muka yi ina ta mamakin kaina ,ɗaya ɓangaren kuma na sakawa Ammy da alkhairi da ta haɗa auren nan...
[29/07 à 09:31] MRS SADAUKI 👑: *IBRAHEEM*
```soldier man```

© Chamsiya Laouali Rabo
#MRS SADAUKI💫✍️

*FCWA ☀️*

#Sadaukarwa ga duk waɗanda suka taɓa rasa wani jigo nasu a soja.Allah jadadda rahama a gare ka Yayana AbduRashid😓

7-8

Kiran sallar farin ne ya tashe ni daga dadaɗan baccin da nake.Ina ware ido na yi tozali da fuskar Maryam kwance kan ƙirjina sai baccinta take,moments ɗinmu na jiya ya dawo min na ɗan yi murmushi ina mamakin kaina .Janye ta na yi na nufi toilet na yi wanka,da na fito na shirya caf cikin jallabiya ruwan ƙasa .Sai da na yi nafiloli sannan na wuce masjid ,bayan mun gamo sallah na dawo gida har yanzu ba ta farka ba.
Blanket ɗin na yaye ina mai kiran sunanta " Mary ? Mary tashi ki yi sallah" ta ware idonta kaɗan kafin ta sake lumshe su har da gyara kwanciya ta ci gaba da baccinta.Na dafe goshi na ce " Ammy kin kawo min aiki" ƙara tashe ta na yi,ta na gunguni ta tashi zaune ni kuma na fita na ɗauki key na je na buɗe mota na ɗauko takardun Daddy ya bani.Ina komawa bedroom na ga ta sake komawa bacci,raina ne na ji ya ɓace cikin ɗaga murya na ce " keee! Tashi na ce har yanzu ba ki yi sallar ba ne ko me"

A firgice ta tashi ta na kuka tare da zuba min manyan idonta," ba za ki wuce ba kenan?" na faɗa ina nufo ta da sauri ta ruga ta shige toilet ina jin ƙarar shower na tabbata wanka take.Falo na koma na soma yin aikina,wani iri nake ji na rasa gane mike damuna ma a yanzu.

MARYAM
```

Wani irin mugun tsoron Ibraheemu ne ya shige ta,duk yadda take da tsiwa sosai take shakkar idonsa.Ta na shiga wanka ta soma yi kamar yadda Ammy ta sanar da ita kullum kafin sallar asubah ta fara yin wanka ta yi kuma brush.Maclean ɗin da ta gani ta matsa ta wanke bakinta,soso ma da nasa ta yi amfani sannan ta fito ta saka rigar sallah ta gabatar.Bayan ta gama ta soma karatun Alkur'ani inda ta iya kafin ta zo wanda Granny ta yi mata,ganin ta na ta yin gargada yasa ta yi shiru kar ta yi saɓo.
Miƙewa ta yi ta gyara shimfiɗar gadon ,ta fesa turare wanda tun jiya Ammy ta nuna mata ma'ajiyarsa.Toilet ma sai da ta je ta wanke ta sannan ta fito ta haye bed sai bacci.

IBRAHEEM
Ina nan zaune ina aiki kiran Ammy ya shigo wayata, Allah na gani abin da yasa ban je na gaishe su tun da asubah ba don kar ta yi min zancen tafiyarta ne.
Kiran na ɗauka ko kafin na ce wani abu ta ce " ka sauko ƙasa" sai kuma ta kashe.
Na ja ajiyar zuciya ina jin wani yanayi kafin na miƙe,sai da na duba bedroom na ga Maryam ta koma bacci sannan na sauka.
Ƴan aiki ke ta faman gyaran falo ana ƙara ƙawata shi ,haka na wuce sai gaishe ni suke.Sashen Granny na wuce da sallama a bakina,bayan na gaishe su ne na maida hankalina ga Ammy.Ta sakar min murmushi ta ce " zan tafi Heemu sai in na dawo wajen suna"
Da sauri na sauke idona ƙasa ina cewa "Ammy don Allah ki zauna"
" Mu je ka sauke ni na hau mota"
Na ɗago a karo na biyu na kalle ta,sam babu alamun wasa kan fuskarta hakan yasa na dubi Granny na ce " don Allah Granny ki sa baki mana"
Ta ce "Baba tun da ta ce tafiya za ta yi na san babu wanda zai canza mata ra'ayi,haka halin Maimuna yake yadda ka san mutanen farko sai shegiyar kafiya "

Ba don na so ba haka na ɗauki ƙaramin trollynta muka fito,har mota Granny ta yi mata rakiya ta na mai cewa " wancan tsohon ya ƙi fitowa haka za ki tafi ba ku yi ban kwana ba"
Ammy ta ce " bai komai Mama ai na yi abin da ya kawo ni" addu'a sosai Granny ta yi kafin mu wuce.Gidan Bus na kai ta don Ammy sam ba ta son doguwar tafiya cikin ƙananun motoci,har muka kai ta na yi min nasiha game da zaman aure da kuma jaddada min girman amana .Har ciki na yi mata rakiya,na kunna mata AC seat ɗinta kafin na fito.Ban baro wurin ba har sai da na ga motarsu ta tashi,ina isa gida lokacin ƙarfe takwas na safe ya buga.Sashen Daddy na duba alamun har yanzu su na ciki ba su fito ba,wani takaici ya rufe ni a haka na haye sama.

★A ɓangaren su Daddy kuwa ya na shiga Zeey ta cika bahon wanka ya shiga kamar wani ƙaramin yaro haka ta yi masa wanka.Daddy irin mazan nan ne masu budurwar zuciya sam bai ganin ya girma shi dai burinsa kawai ya ji shi jikin mace ,a kullum bai gajiya haka kuma bai kwanan banza.Yawan buƙatarsa na ɗaya daga cikin abin da yasa ya yi wa Ammy kishiya don

an yi rashin sa'a ita ba kalarsa ba ce,auren kuma bai je ko ina ba ya mutu haka yake ta aure-aure har Allah ya kawo shi ga Zee wacce ta kasance bazawara ba ta taɓa haihuwa ba fitinarta yasa mijinta ya sake ta.Yanzu kuma da ta auri Daddy sai ta ga kamar tasu ta zo daidai duk da ta fi zaton ta fi shi juriya, wannan kuma har da don ita da sauran ƙarfinta ba ta yi shekarunsa ba.
A wannan daren tamkar sallah haka su Daddy aka ta more aure,sai kace wasu karnai.Sallar asubah ma yau a ɗaki yayi ta,sai wuraren ƙarfe tara suka tashi suka yi wanka Zee ta taimaka masa ya shirya cikin kakinsa na sojoji ta ɗora masa hulla sannan suka fito falo.
Jin ta yake kamar ƙwai ya na jin wata muguwar ƙaunarta,ba don komai ba sai don ta iya jure nauyin buƙatarsa.
Kan dianing suka zauna,da sauri mai kula da lafiyarsa ya matso ya auna abincin da wata na'ura aka tabbatar normal yake ba komai sannan Zee ta zuba musu suka fara ci ta na masa hirar soyayya.
“ In ka tafi zan yi kewar ka sosai Baby ”.
“ Zan dawo ai kar ki damu,duk inda zan je ki na maƙale a birnin zuciyata ” Daddy ya faɗa ya na wani murmushi.Zee ta rausayar da kai ta ce “ banda kallon mata Baby don in ka ce za ka yi min kishiya zan kashe kaina”
Da sauri ya ce “ haba don Allah bari yi min zancen mutuwa,na yi miki kishiya akan me? Sai in canzawa kika yi kika dinga min rowar kan ki”
Ta yi wani fari da ido ta ce “ haba Baby in na yi wa rowa ribar mi zan ci? Ai ni taka ce” cike da murna Daddy ya kamo hannunta ya ce “ Baby kin ci kyautar mota ” Zeey ta yi wani irin ihu tare da rungume shi,daidai nan Granny ta fito a gaban idonta.Ta girgiza kai cike da masifa ta ce “ Allah wadaran naka ya lalace! Yanzu kai Isah mi na faɗa ma?” da sauri Zeey ta janye daga jikinsa ta duƙa har ƙasa ta ce “ ina kwana Mama?”

Ba ta amsa ba sai ci gaba ta yi da cewa “ daga yau ku dinga zama can falon ku kuna cin abinci na soke fitowa nan,in kuma wallahi ka ci gaba zan bar ma gidan ka”

Hankalin Daddy ya tashi don ya tsani fushin Granny,haƙuri ya soma bata kafin ya je ya kama hannunta ya zo ya zaunar da ita kan kujera.Da kansa ya zuba mata abincin cike da kulawa,ita kuwa Granny hakan ba ƙaramin daɗi yayi mata ba.
Ta saki murmushi ta ce “ Allah yi ma albarka ”
“ Amen Mamana ki daɗe ki yi ƙarko,sai kin yi Hajiya Mama uwar shugaban sojoji kike doli a lalaɓa ki a sannu in ba haka ba a tayar da yaƙin duniya na uku” Daddy ke faɗa har da wani sunkuya wa ya na yi wa Granny kirari.Ranta fari ƙal ta kai hannu ta ɗora kan kafaɗar shi ta ce “tashi ya isa haka nan wuce ka tafi aiki kar ka makara”
Sai da Daddy yayi kiran waya ya shaida fitowarsa kafin ya fita,masu take masa baya ne suka yi masa rakiya har motarsa kafin su fice.

Zee kuwa kasa zama ta yi kawai ta miƙe ta bar Granny nan ta na cin abinci.Ɗaki ta wuce,akwatin da ta zuba kayan matanta ta buɗe ta zaɓi waɗanda za ta yi aiki da su na daren yau.Murmushi kan fuskarta ta soma jijiƙa su a gorar ruwa ta na girgiza wa,ita kaɗai ta san irin

tanadin da ta yi wa Daddy.A fili ta ce “ ba dai lamarin nan kake so ba,yau zan fito ma da asalin maitata sai na gana ma baƙar wuya ” sai kuma ta kece da dariya.

IBRAHEEMU

Ina shiga ɗaki ko ta kan takardun ban bi ba na wuce bedroom, doguwar jallabiyar na cire na tsaya iya wandon cikin.Hasken ɗakin na kashe na raɓa gefen Maryam,wannan tiririn da zuciyata ke yi na baƙin cikin Daddy na can da wata baƙar amaryasa nake son na kashe.
Abin da na lura shine kiss na yaye damuwa,ban taɓa sanin haka ba sai jiya da na yi wa Maryam shi.Bakina na ɗora kan lips ɗinta ,tun ina yi a hankali har na soma zaƙewa saboda abubuwan da nake ji su na ratsa ni.Zuciyata ce ta ƙara ƙarfin gudu jin Maryam na mayar min da martani,ba sai an faɗa min ba ita ma koyo take kamar dai ni tun da jiya ne muka fara sanin al'amarin.Kiss ɗin ne na ji bai isa na haɗa da romance,rigar jikinta na yi nasarar cire wa na soma sarrafa ta.Kuka ta soma yi min wannan yasa na mirgina baya ina mayar da numfashi,ta tashi zaune ta ɗauki rigarta ina kallonta na ga ta mayar da abar ta kafin ta dire daga bed ɗin.Sam ban yin ƙoƙarin hana ta ba sai ma haushin kaina da na ji,ƴar ƙanƙanuwa yarinya ta kwance min tunani abun takaicin kuma ƙanwar abokina.Na ja wani numfashi tare da ɗauko pilow na rungume.Shiru na yi ina tunanin kaina ‘ yaushe na samu wannan canji? Sanina dai sai lokacin damina kawai sha'awa ke damuna,ko kuma in an yi ƙololuwar sanyi’ sai kuma na ja tsuki a fili wani sashen zuciyata na bani amsar da ‘ ƙila don yanzu an yi maka aure ne an gama ka da mace ɗaki guda’ da sauri na miƙe na shiga toilet jin abin na sake yin gaba-gaba.
Shower na sakar wa kaina,ina tsaka da wanka na soma jin wayata na ruri.Kiran Ammy ne don waƙarta ta musamman ce,a gaggauce na yi wankan na fito.Ina maida kiran amma ba a ɗauka,gabana ne ya shiga faɗuwa ina shirin aika wani saƙon text ɗinta ya shigo ``` Heemu ƴan ta'adda sun tare motarmu a hanya ba zan iya ɗaukar kira ba don tuni sun sauko mu ƙasa an fara lalubar wasu ma```

Ji na yi kamar an buga min wani ƙaton dutse a kai,da sauri na saka kakina na soja da bindigogi.Jikina har rawa yake,ko kallon inda Maryam take ban yi ba na fita da gudu-gudu.Ina cikin mota na kira Daddy na shaida masa amma yake min zancen banza wai kar na je na jira zai tura sojoji amma ina tuni na soma bibiyar layin Ammy na ƙure gudun mota.

Tsawon lokaci ina sharara gudu kafin kira ya shigo da lambar Ammy,na ɗauka da mamakina sai na ji muryarta ce.“Sun yi tafiyarsu sun gudu! Sun bar mu lokaci guda bayan sun yi mana mugun duka Heemu ” na rumtse ido haɗi da jan wani dogon burki ina sauraren yadda Ammy ke rera kuka,dakyar na ce “ gani nan zuwa Ammy don Allah ki bar kuka ki na ɗaga mini hankali”
“ Kar ka zo Heemu yanzu ai za mu tashi daga nan...” daidai nan kiran ya katse,a ta na'urar da na jona nake bibiyar Ammy na ga sun fara gusawa daga wurin alamun motar ta tafi.Amma duk da haka bai sa na koma ba,haka na ci gaba da gudun kusan a tare muka shiga gidan Bus ɗin ni da motarsu.

Ko jira ban yi ba na nufi motar,ana buɗewa na shiga ciki na riƙo Ammy.Fuskarta ta yi ja sosai ga sawun yatsu nan kwance raɗau,haka na fiddo ta na kai ta motata ina jin haushin kaina.Asibiti na wuce da ita duk ƙoƙarin hana ni da ta yi a cewar ta lafiyarta lau kawai kanta ke ciwo,sai ga shi da muka je asibitin an ce jininta ya hau.Karin ruwa suka saka mata,ina daga gefenta zaune ina saƙar zuci so nake yi na yi mat tambayoyi amma ina jiran har ta dawo hayyacinta.
Kamar ta san abin da nake saƙawa a rai  sai cewa ta yi "sun tafi da wasu daga cikinmu Heemu"
Na dube ta da sauri,idonta na lumshewa take ci gaba da cewa "da dukkanmu za su tafi da mu sai ogansu ya samu kira bayan ya dawo daga wayar ne yake cewa a tafi da iya maza kawai a bar matan"
"Da yayi wayar ba ki ji abin da ya ce ba?"na yi tambayar zuciyata na mugun bugawa,Ammy ta ce "ban ji ba,sai dai lokacin da ɗaya daga cikinsu yake tambayar ogan mi yasa ba za a tafi da mu duka ba sai ya ce umarnin Dagaci ne"
Dagaci babban ɗan ta'adda ne shine shugaban duk wasu manyan-manyan ƴan daba don ƙungiyarsu guda ce. Shiru na yi ina wani tunani haɗi da zargin da ban son ya zama gaskiya ,sai dai duk yadda nake son tunkuɗe zargin abin ya cuttura sai ma wasu abubuwa da suka faru masu kamanceceniya da suka shiga dawo min.
Ganin Ammy ta samu ta yi bacci na miƙe na fita waje na kira lambar Daddy,bugu biyu ya ɗauka kafin ya ce "ina jin ka" sam yanzu babu alamar tashin hankali ba kamar ɗazu da na sanar da shi an kama Ammy kuma gani a hanya zan je ƙwato ta.

"Ya ake ciki ka aika sojojin ne?" na jefo masa tambayar ,shiru yayi bai ce komai ba har sai da na sake maimaita tambayar sannan ya ce "ka ga Abraheemu aiki nake " ƙittt ya katse kiran.Na bi screen ɗin wayar da kallo ina juya maganar Daddyn.Karon farko da na tuna ina da wasu abokai na biyu bayan Abakar ,zama na yi na dinga gwada wayarsu babu wacce ta shiga sai ta mutum ɗaya ya na ɗaga wa ya ce "ya ne Soldier Man ya ƙarin haƙurinmu?"
"Alhamdullah! Shamssudeen don Allah ina son ganin ka akwai aikin da nake son ka yi min"
Ya ce "yanzu dai ina kan hanya mun je Katsina wani aiki sai gobe za mu koma Kano"
Na ɗan nisa na ce "fatan kun yi nasara?"
Ya ce "eh mun kama biyu daga cikin yaran Dagaci"
Da sauri na ce "yaran Dagaci  ka ce?"
Ya ce "eh zuwa jibi za a wuce da su Abuja"
Wani irin daɗi na ji ta faɗi gasasa kenan.Na ce "to kawai zan bari har ku ƙaraso Abujar ido da ido ma za mu fi fahimtar juna" nan muka yi sallama sai a lokacin kawai na je na yi sallolina,Ammy na farkawa na bata jus ta sha magani kafin mu wuce gidanta.....